# RAHOTON

## AYYUKKAN RAYA KASA NA 2018

### A MAZAƁUN TARAYYA DA KE JIHAR ZAMFARA



DA TALLAFI DAGA

MacArthur Foundation

# GABATARWA

Bin diddiƙin ayyukan raya-ƙasa a mazaɓun da ke Jihar Zamfara na daga cikin ayyukan Cibiyar Bincike da Ciyar da Arewa Gaba, wato "Arewa Research and Development Project" (ARDP) wadda Gidauniyar MacArthur ke tallafa wa a ƙarƙashin tsarin shirin tallafi na "On Nigeria 2.0". Ginshiƙin shirin na mayar da hankali ne kan ƙoƙarin hana ƙaruwar cin-hanci da rashawa ta fuskar taimakama shirye-shiryen ƙungiyoyin al'umma na tabbatar da aƙidojin tsare gaskiya da sa hannun al'umma cikin tsarin gudanar da mulki. Babban gurin wannan tsarin aiki shine ya auna ƙarfin sa hannun mutane wajen tantancewa da gudanar da ayyukan raya mazaɓu da kuma yin la'akari da sahihan bukatun al'ummar mazaɓun. Ana kautata zaton cewa wannan tsarin aikin zai kafa matakai ko kuma ya ƙara haɓaka hanyoyin da 'yan ƙasa zasu shiga cikin tsare-tsaren zaɓen ayyukan da kuma sa ido wajen aiwatar da su. Wannan tsarin aikin dai Kungiyar ARDP tare da haɗin guiwar Kungiyar ZamTracka ke jagorantarsa.

Kungiyar ARDP dai wata cibiya ce mai bincike da bata da alaƙa da gwamnati ko la'akari da wata siyasa, ƙabila, ko nuna bambancin addini wadda ayyukanta sun mayar da hankali wajen nazari da tantance manyan matsaloli da ke addabar Arewacin Nijeriya da al'ummarta, da yunƙurin samar da hanyoyin bincike da tsare-tsaren ayyukan da zasu magance matsalolin dake addabar yankin. Gurin Cibiyar shine ƙoƙarin samar da tafarkin bunƙasar tattalin arziki da kyautata rayuwar al'ummar yankin ta hanyoyin da zasu samar da haɗin guiwa tsakanin jama'a da hukomomin gwamnati wajen hada ƙarfi-da-ƙarfe domin ciyar da al'umma gaba.

Ita kuwa ZamTracka, ƙungiya ce mai zaman kan ta da ke Gusau a jihar Zamfar, wadda ta ke yekuwar ganin ana yin taka tsan-tsan da dukiyar jama'a a cikin mulkin jihar. Fitattun ayyukan ta sune samowa da tantance bayanai kan tanade-tanaden ayyuka da ke cikin kasafin kuɗi na jihar Zamfara da kuma ayyukan raya-ƙasa a yankunan mazaɓu, da kuma yin amfani da su wajen wayar da kan al'umma. Manufa dai ita ce a taimaka wa jama'a wajen bin diddiƙin tanade-tanade kasafin kuɗi da yadda ake gudanar da ayyukan raya-ƙasa a mazaɓu. Ana sa ran cewa wannan yunƙuri zai sa a samu masu himma da dagewa wajen ganin ana gudanar da ayyukan raya-ƙasa na gwamnati da hukumominta tare da haɓaka yadda jama'a za su nemi samun ɗorarriyar hanyar tsoma bakinsu a cikin gudanar da al'amuran jiharsu.


# ƘARIN HASKE

Ayyukan raya-ƙasa na mazaɓu wasu ayyuka ne da wakilai a majalisun dokoki na tarayya ke ƙirƙirowa domin kawo ribar mulkin demokaraɗiyya ga al'ummominsu domin haɓakar ci-gaban yankunan karkara. A kan gabatar da bukatun gudanar da waɗannan ayyukan ne ga sashen mulki a lokacin da ake tsare-tsaren kasafin kuɗi. Tsarin mulkin ƙasa ya tanadi cewa majalisun tarayya ke da alhakin sanya ido akan ayyukan gwamnati. Kasancewar 'yan majalisu ne ke ƙirƙirar ayyukan, ashe su ke da nauyin su riƙa yiwa jama'a bayanai akai-akai akan ayyukan. Wannan ya isa hujja saboda talakawa ba za su iya tunkarar hukumomin gwamnati cikin sauƙi ba kamar yadda za su iya tuntuɓar wakilan su. Domin ganin munbi diddiƙin waɗannan ayyukan raya ƙasa akan kari, mun yi amfani da jami'an mu waɗanda suka san wuraren da ake gudanar da takamaiman ayyukan.

A shekarar 2018, an tsara gudanar da ayyyukan raya-ƙasa guda 28 kan jilmilar kuɗi Naira Miliyan dubu ɗaya da miliyan ɗari shidda da tis'in (N1.69bn); waɗanda mafi yawancinsu ba manyan ayyuka bane. Ayyuka 24 daga cikin 28, wanda kuɗinsu ya kai Naira miliyan dubu da ɗari ukku da arba'in (N1.34bn), suna cikin wannan rukunin. Abin al'ajabi shine ayyuka 4 ne kawai manyan ayyuka. Hakan na tabbatar da cewa ba'ayi la'akari da bukantun al'ummar mazaɓu ba, shi yasa mafi yawan ayyukan basu da alaƙa da manyan bukatun mazaɓun. Daɗi-da-ƙari kuma, waɗannan ayyuka na tallafi ba'a iya fayyace yanayin maƙasudinsu kuma wani ba zai iya tantance amfani da kimarsu ba. A bisa ƙoƙarin bin diddiƙin ayyukan shekarar 2018, jami'an mu basu iya tantance kimar irin waɗannan ayyuka ba saboda babu ruhinsu na zahiri a lokacin aikin bin diddiƙin ayyukan.

Bisa la'akari da bayanan da suka gabata, munyi amfani sa tsarin tambayoyi a ƙoƙarin jin ra'ayoyin jama'ar mazaɓu don tabbatar da yiwuwar ko an gudanar da waɗannan ayyuka. Haka kuma abin a fili yake cewa ma fi yawan al'ummomin da ke waɗannan mazaɓu basu da masaniya game da tsarin ayyukan raya ƙasa na mazaɓu ballantana su iya zaɓen ayyukan da suka dace da su. Kusan a dukkan mazaɓun, mutane suna ganin cewa ire-iren waɗannan ayyukan bayar da tallafi wata alfarma ce daga aljifan 'yan majalisunsu. Saboda haka, ma'abotan siyasar 'yan majalisun ne ke cin gajiyar ire-iren waɗannan ayyukan na tallafi.

# DALLA-DALLAR KIDIDDIGAR AYYUKA



# JIMILLAR KUƊI

# N1.69BN

14%

**MANYAN AYYUKA**


N348M

86%

**AYYUKAN TALLAFI**

N1.34BN

# JIMILLAR KASON AYYUKAN DA AKA GUDANAR A CIKIN KASHI ƊARI



# ZAMFARA TA TSAKIYA

JIMILLAR AYYUKA

3

AYYUKAN DA AKA YI

2

AIKIN DA AKE KAN YI

1

AYYUKAN DA BA A GANO BA

0

## GININ KARAMIN FILIN WASA DA KATANGE SHIA 'YANDOTON DAJI, ZAMFARA TA TSAKIYA

Kuɗin Aiki : N90m    Matsayin Aiki: An Aiwatar

'Yandoton Daji wani ƙaramin gari ne a yankin Karamar Hukumar Tsafe, wanda ba shi da tazara mai yawa daga Gusau. Ba amfanin a ce za a gina ƙaramin filin wasa idan aka yi la'akarai da yanayin tsarin tattalin arzikin jama'ar yankin. Yana da matuƙar wahala a iya bada wata ƙwaƙƙwarar hujjar neman yin wannan aikin.

Masu bin diddiƙin yadda ake gudanar da aikin sun fahimci cewa jama'ar wannan gari ba su da masaniyar cewa Gwamnatin Tarayya ce ta bada kuɗin gudanar da wannan aiki. Da yawa cikin al'ummar na ganin cewa karimcin wakilin su ne domin ya samar musu da cibiyar shaƙatawa.

Lokacin da muke duba aikin, mun fahimci cewa an dakatar da aikin tun fiye da shekaru biyu da suka wuce, amma an katange filin an kuma sanya harsashin ginin wurin zaman 'yan kallon wasa. A wajen binciken namu, mun gano cewa har a shekara ta 2019 an sake miƙa wannan aiki akan wasu kuɗin na Naira Miliyan 100. Aikin dai yaci gaba har surar aikin ta fara kankama.








## SAMAR DA ABINCI DAWASU KAYAYYAKI A MATSUGUNAN 'YAN GUDUN HIJIRAA ZAMFARA TA TSAKIYA, KASHI NA 1.

Kuɗin Aiki: N107.142m    Matsayin Aiki: An Aiwatar

A shekararun 2018 da 2019 dai ta'addanci sun yi ƙamari a yankin arewa ma so yammacin Nijeriya, musamman ma a Jihar Zamfara. Wannan lamari ya haifar da matsaloli da ke yin sanadiyyar dubban jama'a suna barin ƙauyuka suna komawa birane, wanda hakan ya haifar da cunkuson da ke barazana a kan yalwar muhimman abubuwan more rayuwa. Wannan ya haifar da buƙatar neman agajin gaggawa daga hukumomin gwamnati da ƙungiyoyin al'umma da kuma iraren ƙungiyoyi masu bada tallafi.

Mun fahimci cewa an rarraba hatsi irin su masara da gero da dawa da shinkafa da sukari da kuma kayayyaki irin su katifu da barguna da tantuna a matsugunan 'yan gudun hijira da ke wurare daban-daban a yankin. Ba mu iya tantance haƙiƙanin kuɗin da aka kashe ko yawan kayyakin ballantana yawan mutanen da sukaci gajiyar tallafin ba. Haka kuma ba mu iya fayyace hanyoyin da aka bi wajen rabon kayayyakin ba.

## SAMAR DA ABINCI DA WASU KAYAYYAKI A MATSUGUNAN 'YAN GUDUN HIJIRA A ZAMFARA TA TSAKIYA, KASHI NA 2.

Kuɗin Aiki: N107.142m    Matsayin Aiki: An Aiwatar

A shekararun 2018 da 2019 dai ta'addanci sun yi ƙamari a yankin arewa ma so yammacin Nijeriya, musamman ma a Jihar Zamfara. Wannan lamari ya haifar da matsaloli da ke yin sanadiyyar dubban jama'a suna barin ƙauyuka suna komawa birane, wanda hakan ya haifar da cunkuson da ke barazana a kan yalwar muhimman abubuwan more rayuwa. Wannan ya haifar da buƙatar neman agajin gaggawa daga hukumomin gwamnati da ƙungiyoyin al'umma da kuma iraren ƙungiyoyi masu bada tallafi.

Mun fahimci cewa an rarraba hatsi irin su masara da gero da dawa da shinkafa da sukari da kuma kayayyaki irin su katifu da barguna da tantuna a matsugunan 'yan gudun hijira da ke wurare daban-daban a yankin. Ba mu iya tantance haƙiƙanin kuɗin da aka kashe ko yawan kayyakin ballantana yawan mutanen da sukaci gajiyar tallafin ba. Haka kuma ba mu iya fayyace hanyoyin da aka bi wajen rabon kayayyakin ba.

# ZAMFARA TA AREWA

JIMILLAR AYYUKA

3

AYYUKAN DA AKA YI

1

AIKIN DA AKE KAN YI

0

AYYUKAN DA BA A GANO BA

2

## SAMAR DAKAYAN NOMADA MAGUNGUNAN ƘWARI GAMANOMAN RANI A YANKUNAN KANANAN HUKUMOMI 4 DAKE AREWACIN JIHAR ZAMFARA.

Kuɗin Aiki: N60m    Matsayin Aiki: An Aiwatar

Waɗanda jami'anmu suka tuntuɓa sun bayyanar da cewa an gudanar da wannan rabon a wani gangami kuma waɗanda suka ci gajiya sun fito daga ƙananan hukumomin Shinkafi, Zurmi, Kaura Namoda da Birnin Magaji. Kayayyakin da aka raba sun haɗa da injunan feshi da magungunan ƙwari da sinadaran inganta iri da kuma taki.

Ba mu da takamaimen bayanin yadda aka zaɓo waɗanda suka ci gajiyar shirin sai dai ga dukkan alama suna da jiɓintaka da 'yan siyasa masu goyan bayan wakilin a Majalisar Tarayya. Ba mu iya tantance yawan waɗanda su kaci gajiyar shirin ba koda yake mun fahimci cewa sun fito daga dukkan mazaɓun na ƙananan hukomomi da ke shiyyar.

## SHIRIN BAYAR DATALLAFIN JARI DOMIN GUDANAR DASANA'O'I GA MATASA DA KE AREWACIN ZAMFARA

Kuɗin Aiki: N25m    Matsayin Aiki: Ba'a sani ba

Masu bin diddiƙin yadda ake gudanar da ayyuka sun zagaya mazaɓar domin samun tabbatar da aiwatar da shirin amma babu wani bayani da ke tabbatar da aiwatar da wannan shirin.

## SAMAR DA BABURA DOMIN RABAWA GA MALAMAN GONA

Kuɗin Aiki: N214.280m    Matsayin Aiki: Ba'a sani ba

Masu bin diddiƙin yadda ake gudanar da ayyuka sun zagaya mazaɓar domin samun tabbatar da aiwatar da shirin amma babu wani bayani da ke tabbatar da aiwatar da wannan shirin.

# ZAMFARA TA YAMMA

JIMILLAR AYYUKA

1

AYYUKAN DA AKA YI

0

AIKIN DA AKE KAN YI

0

AYYUKAN DA BA A GANO BA

1

## SANYA FITILU MASU AIKI DA HASKEN RANA KAN TITI A KAUYUKA MAIMAKON LANTARKI DOMIN BUNKASA NOMAN ITATUWA A ZAMFARA TA YAMMA

Kuɗin Aiki: N214.28m  Matsayin Aiki: Ba'a sani ba

Masu bin diddiƙin yadda ake gudanar da ayyuka sun zagaya mazaɓar domin samun tabbatar da aiwatar da shirin amma babu wani bayani da ke tabbatar da aiwatar da wannan shirin.

# GUSAU/ TSAFE

JIMILLAR AYYUKA

2

AYYUKAN DA AKA YI

2

AIKIN DA AKE KAN YI

0

AYYUKAN DA BA A GANO BA

0

## SHIRIN TALLAFA WA AL'UMMA A GUSAU

Kuɗin Aiki: N75m     Matsayin Aiki: An aiwatar

Wannan mazaɓar ta amfana ne kawai da shirye-shiryen ayyukan tallafi waɗanda mai wakiltar ta daga shekarun 2015 zuwa 2019 ya gabatar. A tsakanin wannan lokacin babu babban aiki guda ɗaya na raya ƙasa da aka gabatar. Rashin takamaimai a laƙabin shirin na nuna irin rufa-rufa dake kunshe da yadda 'yan majalisar ke ƙirƙiro irin waɗannan ayyukan. Irin wannan ne ke hana bin diddiƙin ayyuka domin ba a san yanayi da yawan tallafin da aka bayar ba.

An shaida wa jami'anmu da ke bin diddiƙin ayyuka cewa an gudanar da wannan shiri a Gusau. Kayayyakin da aka raba sun haɗa da injunan niƙa da janaretocin samar da wutar lantarki da kayan yin aski na zamani da kekunan ɗinki da babura da kayan abinci waɗanda suka hada da makaroni da mangyaɗa. Waɗanda kan ci gajiyar ire-iren wannan shirin dai 'yan siyasa ne magoya bayan zaɓaɓɓun wakilai da kuma muƙarraban su. Kuma an ƙara gano cewa mutanen da ke mazaɓu ba su san Gwamnatin tarayya ce ke bayar da kuɗin gudanar da irin waɗannan ayyuka ba wai wakilan su bane kamar yadda su kan ɗauka a bisa kan rashin sani.

## SHIRIN TALLAFA WA AL'UMMA A TSAFE

Kuɗin Aiki: N75m     Matsayin Aiki: An aiwatar

Wannan mazaɓar ta amfana ne kawai da shirye-shiryen ayyukan tallafi waɗanda mai wakiltar ta daga shekarun 2015 zuwa 2019 ya gabatar. A tsakanin wannan lokacin babu babban aiki guda ɗaya na raya ƙasa da aka gabatar. Rashin takamaimai a laƙabin shirin na nuna irin rufa-rufa dake kunshe da yadda 'yan majalisar ke ƙirƙiro irin waɗannan ayyukan. Irin wannan ne ke hana bin diddiƙin ayyuka domin ba a san yanayi da yawan tallafin da aka bayar ba.

An shaida wa jami'anmu da ke bin diddiƙin ayyuka cewa an gudanar da wannan shiri a Gusau. Kayayyakin da aka raba sun haɗa da injunan niƙa da janaretocin samar da wutar lantarki da kayan yin aski na zamani da kekunan ɗinki da babura da kayan abinci waɗanda suka hada da makaroni da mangyaɗa. Waɗanda kan ci gajiyar ire-iren wannan shirin dai 'yan siyasa ne magoya bayan zaɓaɓɓun wakilai da kuma muƙarraban su. Kuma an ƙara gano cewa mutanen da ke mazaɓu ba su san Gwamnatin tarayya ce ke bayar da kuɗin gudanar da irin waɗannan ayykan ba wai wakilan su bane kamar yadda suke ɗauka a bisa kan rashin sani.

# MARU/ BUNGUDU

JIMILLAR AYYUKA

3

AYYUKAN DA AKA YI

2

AIKIN DA AKE KAN YI

0

AYYUKAN DA BA A GANO BA

1

## SAMAR DA BABURA A MARU/BUNGUƊU

Kuɗin Aiki: N38.4m    Matsayin Aiki: An aiwatar

Kusan dukkan wannan mazaɓa karkara ce, ba ta da hanyoyi masu kyau, ga rashin wutar lantaki da rashin ruwan famfo. Tunanin rarraba babura ga al'ummar da bata da waɗannan abubuwa more rayuwa bai yi la'akari da manyan bukatu da matsalolin mutanen wannan mazaɓa ba.

An ce an gabatar da wannan shirin a cikin yankin Karamar Hukumar Maru, inda aka sawo baburan aka kuma rarraba a mazaɓu da ke ƙaramar hukumar. Ba mu iya tantance waɗanda suka ci gajiyar shirin ba ballantana tsarin rabon.

## SAMAR DA BABURA A MARU/BUNGUƊU

Kuɗin Aiki: N37m    Matsayin Aiki: An aiwatar

Kusan dukkan wannan mazaɓa karkara ce, ba ta da hanyoyi masu kyau, ga rashin wutar lantaki da rashin ruwan famfo. Tunanin rarraba babura ga al'ummar da bata da waɗannan abubuwa more rayuwa, bai yi la'akari da manyan bukatu da matsalolin mtanen wannan mazaɓa ba.

An ce an gabatar da wannan shirin a cikin yankin Karamar Hukumar Bunguɗu, inda aka sawo baburan aka kuma rarraba a mazaɓu da ke ƙaramar hukumar. Ba mu iya tantance waɗanda suka ci gajiyar shirin ba ballantana tsarin rabon.

## KOYAR DASANA'O'I GAMATASADAMATAAMARU/ BUNGUƊU

Kuɗin Aiki: N50M   Matsayin Aiki:Ba'a sani ba

Masu bin diddiƙin yadda ake gudanar da ayyuka sun zagaya mazaɓar domin samun tabbatar da aiwatar da shirin amma babu wani bayani da ke tabbatar da aiwatar da wannan shirin.

# ANKA/ MAFARA

JIMILLAR AYYUKA

3

AYYUKAN DA AKA YI

0

AIKIN DA AKE KAN YI

0

AYYUKAN DA BA A GANO BA

3

## TALLAFIN SHIRYA FINA-FINAI GA MATASA DA MATA A ANKA/MAFARA

Kuɗin Aiki:**N52.24m** Matsayin Aiki: **Ba'a sani ba**

Babu wata fuska da za'a iya kuranta wannan shiri a cikin jiha kamar Zamfara wadda ke fama da bala'in ta'addancin kamar shekaru goma. Kuma ma abin akwai ɗaure kai ganin cewa babu wata sananniyar sana'ar yin fina-finai a cikin jihar.

Wata ƙila tsarin gabatar da wannan shirin wata dabara ce ta karkatar da kuɗin jama'a a ayyukan bogi. Hakan na iya tabbata ganin cewa babu mutum ko guda da ya amfana da shirin wanda masu bin diddiƙin aiki suka tantance a duk faɗin mazaɓar.

## SHIRIN TALLAFA WA MATASA DA MATA A ANKA / MAFARA

Kuɗin Aiki: **N36.24m** Matsayin Aiki: **Ba'a sani ba**

Wannan ma na iya zama hanya ta karkatar da dukiyar jama'a ta hanyar ayyukan bogi. Hakan na iya tabbata ganin cewa babu mutum ko guda da ya amfana da shirin wanda masu bin diddiƙin aiki suka tantance a duk faɗin mazaɓar.

## SHIRIN TALLAFA WA MATASA DA MATA A ANKA / MAFARA

Kuɗin Aiki: **N36.76m** Matsayin Aiki: **Ba'a sani ba**

Wata hanyar ta karkatar da dukiyar jama'a ta hanyar ayyukan bogi. Hakan na iya tabbata ganin cewa babu mutum ko guda da ya amfana da shirin wanda masu bin diddiƙin aiki suka tantance a duk faɗin mazaɓar.

# BAKURA/ MARADUN

JIMILLAR AYYUKA

4

AYYUKAN DA AKA YI

1

AIKIN DA AKE KAN YI

0

AYYUKAN DA BA A GANO BA

3

## HORAR DA MATASA TACE FINA-FINAI A BAKURA/ MARADUN

Kuɗin Aiki: N23m    Matsayin aiki: An aiwatar

Idan an yi la'akari da matsin tattalin arziki da ke addabar yankin, za a ga cewa wannan aiki ɓarnar dukiya ce. Daɗi-da-ƙari, babu wata fitacciyar sana'ar yin fina-finai da har za a bukaci wannan shiri. Tsari da aka bi wajen zaɓo waɗanda suka ci gajiyar shirin zai yi wuyar a tabbatar da shi. A fili yake cewa ba'a tantance bukatun jama'a ba wajen gabatar da wannan aiki.

Ma'aikanta da suka bi sawun wannan aiki sun fahimci cewa an zaɓo waɗanda suka ci gajiyar aikin daga sassan mazaɓar. An gudanar da lacca na yini ɗaya kan muhimman abubuwa da suka shafi harkar shirya fina-finai da kuma tace su, inda a ƙarshen shirin aka bai wa kowane daga cikin mahalartan Naira dubu ashirin (N20,000).

## HORAR DA MANOMAN KARKARA A KAN NOMAN SHINKAFA

Kuɗin Aiki: N40m    Matsayin Aiki: Ba'a sani ba

Masu bin diddiƙin ayyuka sun zagaya mazaɓar domin ƙoƙarin tabbatar da ko an gudanar da shirin amma babu wani bayanin da ya tabbatar da aiwatar da aikin.

## HORAR DA MANOMAN KARKARA A KAN NOMAN GERO

Kuɗin Aiki: N40m    Matsayin Aiki: Ba'a sani ba

Masu bin diddiƙin ayyuka sun zagaya mazaɓar domin ƙoƙarin tabbatar da ko an gudanar da shirin amma babu wani bayanin da ya tabbatar da aiwatar da aikin.

## HORAR DA MATASA DA MATA A KAN NOMAN DAWA

Kuɗin Aiki: N22.24m    Matsayin Aiki: Ba'a sani ba

Masu bin diddiƙin ayyuka sun zagaya mazaɓar domin ƙoƙarin tabbatar da ko an gudanar da shirin amma babu wani bayanin da ya tabbatar da aiwatar da aikin.

# SHINKAFI/ ZURMI

JIMILLAR AYYUKA

4

AYYUKAN DA AKA YI

0

AIKIN DA AKE KAN YI

0

AYYUKAN DA BA A GANO BA

4

## BAYAR DABABURAN YIN HAYA DONBUNKASA SANA'AA SHINKAFI/ ZURMI

Kuɗin Aiki: N13.24m     Matsayin Aiki: Ba'a sani ba

Masu bin diddiƙin ayyuka sun zagaya mazaɓar domin ƙoƙarin tabbatar da ko an gudanar da shirin amma babu wani bayanin da ya tabbatar da aiwatar da aikin.

## KOYAR DA SANA'O'I DA BAYAR DA TALLAFI A SHINKAFI/ ZURMI

Kuɗin Aiki: N42m     Matsayin Aiki: Ba'a sani ba

Masu bin diddiƙin ayyuka sun zagaya mazaɓar domin ƙoƙarin tabbatar da ko an gudanar da shirin amma babu wani bayanin da ya tabbatar da aiwatar da aikin.

## KOYAR DA MATSAKAITAN HARKOKIN KASUWANCI DA SAMAR DA BABURA A SHINKAFI/ ZURMI

Kuɗin Aiki: N40m     Matsayin Aiki: Ba'a sani ba

Masu bin diddiƙin ayyuka sun zagaya mazaɓar domin ƙoƙarin tabbatar da ko an gudanar da shirin amma babu wani bayanin da ya tabbatar da aiwatar da aikin.

## HAKA RIJIYOYIN BURTSATSE A SHINKAFI/ ZURMI

Kuɗin Aiki: N30m     Matsayin Aiki: Ba 'a sani ba

Daga taken shirin, za'a iya yaba wa ƙudurin wannan aikin a bisa la'akari da muhimmancin sa ga wannan mazaɓa.

Amma abin takaici, masu bin diddiƙin ayyuka sun zagaya mazaɓar domin ƙoƙarin tabbatar da ko an gudanar da shirin amma babu wani bayanin da ya tabbatar da aiwatar da aikin.

# KAURA/ B/MAGAJI

JIMILLAR AYYUKA

2

AYYUKAN DA AKA YI

0

AIKIN DA AKE KAN YI

0

AYYUKAN DA BA A GANO BA

2

## SHIRIN BAYAR DA TALLAFI A KAURA/ BIRNINMAGAJI

<u>KuɗinAiki:</u> N65m <u>Matsayin Aiki:</u> Ba'a sani ba

Taken wannan shiri kaɗai na da ruɗarwa kuma ya wahalar wajen bin diddiƙi domin babu kima ko nau'in tallafin da za'a bayar.

Masu bin diddiƙin ayyuka sun zagaya mazaɓar domin ƙoƙarin tabbatar da ko an gudanar da shirin amma babu wani bayanin da ya tabbatar da aiwatar da aikin.

## SHIRIN TALLAFA WA MATA A KAURA/ BIRNIN MAGAJI

<u>KuɗinAiki:</u> N60.24m <u>Matsayin Aiki:</u> Ba'a sani ba

Taken wannan shiri kaɗai na da ruɗarwa kuma ya wahalar wajen bin diddiƙi domin babu kima ko nau'in tallafin da za'a bayar.

Masu bin diddiƙin ayyuka sun zagaya mazaɓar domin ƙoƙarin tabbatar da ko an gudanar da shirin amma babu wani bayanin da ya tabbatar da aiwatar da aikin.

# GUMMI/ BUKKUYUM

JIMILLAR AYYUKA

3

AYYUKAN DA AKA YI

0

AIKIN DA AKE KAN YI

0

AYYUKAN DA BA A GANO BA

3

## SHIRIN BAYAR DA TALLAFI GA MATASA DA MATA A GUMMI/ BUKKUYUM

Kuɗin Aiki: N60m        Matsayin Aiki: Ba'a sani ba

Taken wannan shiri kaɗai na da ruɗarwa kuma ya wahalar wajen bin diddiƙi domin babu kima ko nau'in tallafin da za'a bayar.

Masu bin diddiƙin ayyuka sun zagaya mazaɓar domin ƙoƙarin tabbatar da ko an gudanar da shirin amma babu wani bayanin da ya tabbatar da aiwatar da aikin.

## SHIRIN BAYAR DA TALLAFI GA MATASA DA MATA A GUMMI/ BUKKUYUM

Kuɗin Aiki: N50m        Matsayin Aiki: Ba'a sani ba

Taken wannan shiri kaɗai na da ruɗarwa kuma ya wahalar wajen bin diddiƙi domin babu kima ko nau'in tallafin da za'a bayar.

Masu bin diddiƙin ayyuka sun zagaya mazaɓar domin ƙoƙarin tabbatar da ko an gudanar da shirin amma babu wani bayanin da ya tabbatar da aiwatar da aikin.

## SHIRIN NOMAN BAN-RUWA A GUMMI/ BUKKUYUM

Kuɗin Aiki: N13.24m        Matsayin Aiki: Ba'a sani ba

Masu bin diddiƙin ayyuka sun zagaya mazaɓar domin ƙoƙarin tabbatar da ko an gudanar da shirin amma babu wani bayanin da ya tabbatar da aiwatar da aikin.

# MANYAN KALUBALEN DA AKA FUSKANTA WAJEN TANTANCE AYYUKAN RAYA-KASA A MAZUƁU NA SHEKARAR 2018

MATSALAR TSARO
Jihar Zamfara na daga cikin wuraren da ayyukan ta'addanci suka yi ƙamari a Arewa ma-so Yammacin Nijeriya. Wannan matsalar ta hana ma'aikanmu tuntuɓar al'ummomin da ke mazaɓu game da bin sawun ayyukan raya ƙasa. Muna fatar sha'anin tsaro zai kyautatu.

BAYAR DA FIFIKO GA KANANAN AYYUKAN DA KE DA WAHALAR BIN DIDDIKINSU
Ayyukan alfarma na tallafi abubuwa ne na wucin-gadi da zasu iya biyan bukatu na ɗaiɗaikun mutane ba tare da share hawayen alumma ba sune suka fi yawa a nan. Ma'aikatanmu sun fuskanci ƙalubalen bin sawu da tantancesu saboda babu wani cikakken tsari da aka samar na zaɓen mutanen wanda a hasali ma mafi yawan waɗanda suka ci gajiyar ayyukan ma'abutan siyasa ne ba waɗanda ke da matuƙar bukatar agaji ba.

RASHIN TSARIN JIN RA'AYI DA TANTANCE BUKATUN JAMA'A
Ɗaya daga cikin ƙalubale a dangane da ingancin ayyukan raya-ƙasa na mazaɓu shine rashin samun sahihan bayanai akan ayyukan da rashin tsarin wayar da kai tare da tsoma al'ummomi cikin zaɓensu da kuma gudanar da su. Don haka ne, ma fi yawan ayyukan basu da alaƙa da manyan bukatun mutanen mazaɓun.

## ABIN DA AKA FAHIMTA DA KUMA MATAKIN DA ZA MU ƊAUKA

Mun fahimci cewa babu fitaccen tsarin biyan kuɗaɗen waɗannan ayyuka kuma ana biya ne guntu-guntu wanda kesa kuɗin su shiga cikin wata shekarar kasafin kuɗi. Hakan kan haifar da giɓi game da yadda ake bayar da kuɗaɗen gudanar da ayyukan. Samun sahihan bayanai na ayyuka na da muhimmanci domin yin yekuwa da zata ƙara sa kulawa wajen tsare gaskiya da riƙon amana.

Saboda haka, idan an yi la'akari da ire-iren ƙalubalen da aka ambata, zamu yi amfani da dokar 'yancin samun bayanai ta shekarar 2011 domin neman bayanai da suka shafi sarrafa kuɗi daga wajen hukumomin da ke gudanar da ayyuka. Haka zai bamu damar yayata shirin wayar da kai game da ayyuka da aka bayar da kuɗin gudanar da su domin gaggauta kammala su ko kuma yin ƙorafi kan waɗanda aka yi watsi da su ko aka ƙi aiwatar da su. Haka kuma zai bayar da dama ga jama'a da ke mazaɓu wajen neman bayanai daga wakilansu da kuma tabbatar da samun nagartattun ayyukan more rayuwa a cikin mazaɓu.

# A TAKAICE...

### TUNTUBAR AL'UMMA

Tunda yake maƙasudin gudanar da ayyukan raya-ƙasa a mazaɓu shi ne a tabbatar da al'ummomin da ke karkara sun ci moriyarsu, ya wajaba ga wakilan su tuntuɓi al'ummomin mazaɓunsu a lokacin tsare-tsaren aiwatar dasu domin ganin an sanya muhimman abubuwan da suke bukata a mazaɓun.

### TSARA KASAFIN KUƊI DA CIKAKKUN BAYANAI

Akwai bukatar sanya sunayen wuraren da za'ayi ayyukan a cikin tsarin kasafin kuɗi, domin yadda jama'a da ƙungiyoyi zasu iya samun bayanai. Kamar yadda muka lura a mafi yawan ayyukan za'a samu tsari da sunan aiki da yawan kudi amma babu cikakken bayani a kan wurin da za'ayi aiki. Irin wannan tsari ne ke bayar da dama a karkatar da kuɗaɗe domin cin-hanci da rashawa.

**N1.13bn**

Aka kasafta ga ayyukan da ba'a iya tababar da gudanar da su

**N551m**

Haƙiƙanin kuɗaɗen da aka kashe na ayyukan raya-ƙasa a mazaɓun da ke Jiha.

ZamTracka

Data | Civic Advocacy | Social Accountability

Follow up and track implementation of public projects within your vicinity

Upload pictures, add comments, send feedback to institutions

Announce and share with your friends, family and thousand across the state

Continue to engage.

No. 40, Sadiqu Sadiq Road,
Tudun Wada, Gusau, Zamfara State.

f/t @ZamTracka

ZamTracka@gmail.com

# #AskQuestions